## SŪRATUSH SHARḤ سُورَةُ الشَّرۡحِ

Tana karantar da ni'imõmin da Allah Ya yi wa Annabi, tsĩra da amincin Allah su tabbata a gare shi, game da sifõfinsa, dõmin Ya gina wasu hukunce-hukunce a kansu.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

| | |
|---|---|
| *1.* Ashe, ba Mu būɗa maka zũciyarka ba (dõmin ɗaukar haƙuri da fahimta)? | أَلَمۡ نَشۡرَحۡ لَكَ صَدۡرَكَ ١ |
| *2.* Kuma Muka saryar maka da nauyinka, | وَوَضَعۡنَا عَنكَ وِزۡرَكَ ٢ |
| *3.* Wanda ya nauyayi bãyanka? | ٱلَّذِيٓ أَنقَضَ ظَهۡرَكَ ٣ |
| *4.* Kuma Muka ɗaukaka maka ambatonka? | وَرَفَعۡنَا لَكَ ذِكۡرَكَ ٤ |
| *5.* To, lalle ne tãre da tsananin nan akwai wani sauƙi, | فَإِنَّ مَعَ ٱلۡعُسۡرِ يُسۡرًا ٥ |
| *6.* Lalle ne tãre da tsananin nan akwai wani sauƙi. | إِنَّ مَعَ ٱلۡعُسۡرِ يُسۡرًا ٦ |
| *7.* Sabõda haka idan ka ƙãre (ibãda) sai ka kafu (kana rõƙon Allah). | فَإِذَا فَرَغۡتَ فَٱنصَبۡ ٧ |
| *8.* Kuma zuwa ga Ubangijinka ka yi kwaɗayi. | وَإِلَىٰ رَبِّكَ فَٱرۡغَب ٨ |